

Taimakawa Zaɓaɓɓu na Allah

Yesu ya ɗauki kunyarmu domin mu sami ɗaukakar Sa



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Ni da matata mun taɓa taimaka wa matan Yahudawa biyu waɗanda suka tsere daga Sobiet a Rasha. A taƙaice dai, waɗannan matan sun nemi jinƙan mu. Mun shiga wahala da matsala sosai domin taimaka masu, kuma, ta wurin alherin Allah, a ƙarshe mun sami nasarar yin hakan. Wata rana, ina cikin damuwa yayin da nake hawa wani tudu mai tsayi a Haifa saboda su. Akwai zafin rana, kuma, ko da yake waɗannan matan suna godiya sosai a koyaushe, na yi tunanin cewa wannan babbar nawaya ce nake sha saboda su. Sai Allah ya ba ni wannan ayar; Ban san inda zan gano ta a cikin Littafi Mai Tsarki a lokacin ba, amma kalmomin sun zo mani kawai:

> "Ina fa daurewa da dukan abu sabili da zaɓaɓɓu [zaɓaɓɓun Allah], domin su kuma su sami ceton da ke cikin Kristi Yesu tare da daraja ta har abada." (2 Timotawus 2:10)

Daga wannan ɗandanon, sai na ga cewa matsayina ya yi nisa da na Yesu a kan gicciye. Wahalar da nake sha ba ta kai yawan a kwatanta ta ba. Amma manufar ita ce taimakon zaɓaɓɓu na Allah su sami ceto da ɗaukaka ta har abada.

Dukanmu muna buƙatar lokaci domin yin tunani a kan wannan kalma ɗaukaka, domin ita ce ƙarshen mu. Idan akwai abin da za a biya domin ɗaukaka, to, ku yarda da ni, wannan ya cancanci hakan. Za a iya buƙata a wani lokaci mu bar waɗannan gumakan biyu na walwala da jin daɗi. Idan da za mu iya samun hangen gaba na ganin sakamakon rashin walwala da sadaukarwar mu, wata rana za mu ga mutane cikin ɗaukaka waɗanda suka kai can saboda abin da muka yi.

Wannan shi ne abin da ya ƙarfafa Yesu ya yi hakan. Bai yi hakan domin kansa ba, amma domin ya kawo 'ya'ya da yawa ne zuwa ga ɗaukaka.

Na gode maka, Yesu, saboda aikin ka a kan gicciye. Ina furta cewa zan bar waɗannan gumaka biyu na walwala da jin dadi, kamar yadda Yesu ya yi, don taimakawa wajen ceto zaɓaɓɓu na Allah. Yesu ya ɗauki kunyata domin in sami ɗaukakar Sa. Amin.

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-138-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.